## OPT-SMC Training videos 2021

## Matakan Bada Maganin Zazabin Cizon Sauro A Lokacin Damuna Wato SMC

| S/No. | Transcript in Hausa |
|---|---|
| 1 | Bayan kammala kallon wannan bidiyo, za a fahimci yadda za a bayar da maganin zazzabin cizon sauro na lokacin damuna mai suna Seasonal Malaria Chemoprevention wato SMC ga yara domin kare su daga wannan cutar. |
| 2 | A wannan shekara, saboda annobar Korona (Covid-19), dole kowanne jami'in kiwon lafiya ya fito a kimtse, ta hanyar sanya safar hanci da kuma gujewa shiga cikin mutanen gidan sosai domin kareyar da wannan cuta. |
| 3 | Da zarar jami'i ya shiga kowanne gida, ya gabatar da kansa da kuma abokin aikinsa a matsayin jami'an lafiya daga hukumar lafiya ta yankin, kuma sun zo domin bada maganin kariya mai muhimmanci daga cutar cizon sauro na yara. |
| 4 | A tabbatar an bada tazara tsakanin jami'ai da kuma masu karbar magani a ko yaushe. |
| 5 | A wanke hannu. |
| 6 | Daga nan sai a fara bada magani.<br><br>A nemi wuri a zauna, a kuma bukaci masu gida su bada kofi, cokali da tsaftacaccen ruwan sha. |

| | |
|---|---|
| 7 | A fito da kayan aiki kamar haka:<br>✓ Katin maganin SMC<br>✓ Katin shaidar bada maganin SMC<br>✓ **Idan kuna rikodin maganin SMC ta hanyar dijital** bayanan bada magani, dole a bude manhajar a waya ko tabulet.<br>Iddan ba bukatar dijital a dauki bayanan ba, ana bukatar:<br>✓ Takardar rijistar maganin SMC<br>✓ da Takardar kirge |
| 8 | Idan wannan shi ne karon ka na farkon zuwa wannan gidan a cikin shekarar nan, ka bukaci ganin dukkan yaran da suke wannan gida yan kasa da shekara biyar kuma a dauki bayanansu a takardar rijistar maganin SMC ko kuma a na'ura.<br>Idan yaro ko yarinya dan kasa da wata uku ne, BA ZA a ba shi maganin SMC ba a yayin wannan ziyara, amma za a iya bayarwa a ziyara ta gaba. Saboda haka a tabbata an yi musu rijista.<br>Wannan ya na taimakawa wajen tabbatar da cewa ba a tsallake kowanne yaro ba ko yarinya a ziyara ta gaba. |
| 9 | A tabbata an cika katin bayanan yaran da aka baiwa maganin (SMC Record Card) ga kowanne yaro da ya isa karbar maganin. |
| 10 | A rubuta suna da sauran bayanan yaron. A kuma dauki bayanan bayar da magani BAYAN an gama ba wa yaron maganin SMC. |
| 11 | Kafin a fara bada maganin, a tabbata yaron ya isa a bashi maganin SMC. |

| | |
|---|---|
| 12 | Mataki na farko, a tabbatar da shekarun yaron.<br><br>Idan iyaye ko masu kula da yaron ba su san ainihin shekarunsa ba, a nemi takardar rigakafin yaron domin tabbatarwa ko kuma a tambayi sauran mutanen da suke cikin gidan. |
| 13 | Kada a baiwa yaron da bashi da ishashshiyar lafiya maganin SMC. A garzaya da shi cibiyar kiwon lafiya ko jami'in kiwon lafiya mafi kusa domin gwaji. |
| 14 | Idan yaron na fama da zazzabin cizon sauro ne, za a bashi kulawar A-C-T. |
| 15 | Idan yaron ya sami wata matsala sakamakon shan maganin SMC ko wasu magungunan daban a baya, to kada a bashi SMC. |
| 16 | A bincika ko yaron ya sha wani magani a cikin mako hudu (4) da suka shude. |
| 17 | Idan yaron ya sha SP ko AQ (na zazzabin cizon sauro) ko kuma Bactrim ko Cotrimoxazole (na kwayoyin cuta), ba za a bashi SMC a wannan rana ba. |
| 18 | Bayan an tabbatar da cewa yaro ya cancanta bayan duba ga matakai na baya, an iya ci gaba da ba shi maganin SMC. |
| 19 | A zabi samfuri ko katin maganin SMC da ya dace da shekarun yaron. |
| 20 | A ɗora katin maganin a kan kujera ko tebur. |
| 21 | A sanar da mai kula da yaron cewa za ta bawa yaron kwayoyi biyun na farkon katin maganin. |

| | |
|---|---|
| 22 | Sai a ce ma mai kula su zuba ruwa dan kadan, a hankali kuma yadda zai shanye kan maganin. Za a iya bukatar a dama maganin domin ya narke. |
| 23 | A tabbatar da yaron idon sa biyu, sannan a zaunar da shi da kyau.<br><br>A nuna wa mai kula da yaron yadda zata bada maganin a hankali, a kuma tabbatar da yaron ya hadiye maganin gaba daya.<br><br>Sannan a dauraye kofin da ruwa kadan, a bawa yaron ya kuma hadiye wa, har sai ya gama shan duka.<br><br>Sai a dan jira zuwa wani lokaci domin a tabbatar yaron lafiyarsa kalau. |
| 24 | A gayawa mai kula da yaron cewa idan yaron ya amayar da maganin kafin minti 30 da aka ba shi, za a iya kara ba da maganin.<br><br>Su neme ka, ka kuma basu wani sabon katin maganin tare da karbar tsohon domin zubarwa.<br><br>Idan yaron ya kara amayarwa a karo na biyu, to a shigar da wannan bayani a manhajar daukar bayanai ta waya ko tabulet. Kuma kar a kara ba shi maganin. |
| 25 | Bayan an kamala cika katin bayanan SMC, a ajiye shi a matsa gefe yadda mai kula da yaron zasu iya daukawa.<br><br>Wannan katin SMC na bayanar da mai kula da yaron ne kuma yana dauke da bayanin shan maganin yaron.<br><br>Idan kana amfani da takardar kirge, a tabbata an shigar da adadin yaran da aka bawa magani a wannan ziyara. |
| 26 | A yi wa masu kula da yaron bayanin yadda za a bawa yaron ragowar magungunan: Kwaya daya gobe, sannan na karshen kuma jibi. Gaba daya magungun a cikin kwana uku ake shanye su. |

| | |
|---|---|
| 27 | A godewa masu gidan domin yarda da suka yi wajen karbar wannan magani kuma a tuna musu wadannan muhimman sakonni:<br><br>✓ Su tuna ranar da jami'an lafiya za su kara dawowa.<br><br>✓ A ajiye katin maganin a wuri mara danshi in da yara baza su iya dauka ba.<br><br>✓ A tabbata an shanye maganin gaba daya kamar yadda aka tsara. Kada a bawa wani daban maganin<br><br>✓ Maganin SMC bashi da illa, amma idan dai har yaro ya nuna alamun samun matsala bayan ya sha maganin, to a hanzarta a kai shi cibiyar kiwon lafiya.<br><br>✓ Maganin SMC yana bada kariya na wata guda ne, wato makonni hudu. Dole a ci gaba da shan wannan magani a watanni na gaba har zuwa wata hudu.<br><br>✓ Kowa a gidan ya dinga bacci cikin gidan sauro mai dauke da magani (mosquito net)<br><br>✓ A gaya wa masu kula su wanke hannayensu da zarar kun fita daga gidan. |
| 28 | Muna muku godiya da kuka kasance tare da mu har zuwa karshen wanna bidiyon.<br><br>Yanzu zaku iya bawa yara kyakyawar garkuwa daga ciwon zazzabin cizon sauro ta hanyar maganin SMC. |